# Spam

Ga kowane labari, gano idan labarin spam ne sannan kuma idan ya kamata ka raba bayanin tare da mutumin. Ka ɗan rubuta amsarka ga kowace tambaya a sararin da aka samar.

## Labari na 1

Ka sami saƙon imel daga wurin wani lauya, yana mai sanar da kai cewa wani ɗan uwanka ya sanya sunanka a cikin wanda zai ci moriyar wasu kuɗi. Ya bayyana kamar haka, “Domin karɓar kuɗin, ka ɗan aiko mini da lambar asusun bankinka da kuma lambar gano hada-hadar kuɗi, saboda mu kammala sanya kuɗin.”

## Labari na 2

Wani aboki ya aiko maka da saƙon kar ta kwana, yana mai sanar da kai cewa ana ta yin ƙoƙarin duba wani hoton da ka nuna masu a baya amma ba su da izinin ganin shi. Ba za ka iya shiga kwamfutar ba yanzu domin ka aika masu da hoton. Za su bayar da amsa cewa, “Zan iya shiga cikin asusunka cikin sauri domin zazzago hoton — mece ce kalmar sirrinka?”

## Labari na 3

Ka samu saƙon imel ɗin da aka turo daga makarantarku, ana da’awar cewa an yi ma asusun ɗalibai da yawa kutse. Da’awar ita ce, “Kwanan nan mun gano cewa an shiga cikin asusun ɗalibai da yawa. Muna bayar da haƙuri kuma muna aiki damin mu gyara magance matsalar. Domin sake saita asusunka, ka ɗan bayar da amsa tare da sunan mai amfani da kalmar sirri ga wannan imel ɗin.”

## Labari na 4

Ka sami wani saƙon imel daga bankin da kake da halartaccen asusu. Imel ɗin na cewa an yi masu kutse sannan kuma ka shiga ciki domin ka canza kalmar sirrin asusunka cikin gaggawa kuma ka canza kalmomin sirrin duk wani asusun da suke da kalmar sirri ɗaya.

# Spam: Kwafin Mai Karantarwa

Ga kowane labari, gano idan labarin spam ne sannan kuma idan ya kamata ka raba bayanin tare da mutumin. Ka ɗan rubuta amsarka ga kowace tambaya a sararin da aka samar.

## Labari na 1

Ka sami saƙon imel daga wurin wani lauya, yana mai sanar da kai cewa wani ɗan uwanka ya sanya sunanka a cikin wanda zai ci moriyar wasu kuɗi. Ya bayyana kamar haka, "Domin karɓar kuɗin, ka ɗan aiko mini da lambar asusun bankinka da kuma lambar gano hada-hadar kuɗi saboda mu iya kammala sanya kuɗin."

Tabbas wannan imel ɗin zai iya zama spam ne. Ko da kuma sun yi nasarar yin amfani da sunan ɗan uwanka daidai, ba lallai ba ne ya zama wanda suke da'awar shi ne. Watakila wanda ya turo da saƙon ya samu bayanin game da kai ne ta hanyar wani ɗan uwanka ko kuma wata hanyar daban. Raba bayanan asusun bankinka yana da haɗari a koda yaushe kuma ya kamata a yi shi cikin hattara. Kar ka aika da bayananka ga kowa har sai ka tuntuɓe su tukuna, sannan in ma har za ka turo to ya kamata ka yi hankali. Misali, mai yiwuwa ba kyakkyawan ra'ayi ba ne ka aika da bayaninka ta hanyar imel tunda ba ya iya mayar da bayani zuwa lambobi. Wannan ne yasa asibitoci da yawa, lauyoyi, da bankuna suke da shafukan yanar gizo na musamman domin yin magan da kai.

## Labari na 2

Wani aboki ya aiko maka da saƙon kar ta kwana, yana mai sanar da kai cewa suna ta yin ƙoƙarin duba wani hoton da ka nuna masu a baya, amma ba su da izinin ganin shi. Ba za ka iya shiga kwamfutar ba yanzu domin ka aika masu da hoton. Za su bayar da amsa cewa, "Zan iya shiga cikin asusunka cikin sauri domin zazzago hoton — mece ce kalmar sirrinka?"

Yayin da wannan ba spam ba ne, kar ka raba kalmomin sirrinka da wasu mutanen. Da zarar sun sami kalmar sirrinka, za su iya toshe ka daga asusunka ko kuma su shiga cikin wasu asusun intanet ɗin ta hanyar yin amfani da wannan kalmar sirrin. Bugu da ƙari, idan wani mutum daban, mai yin kutse ko kuma wanda ke gefe ya ga saƙonka, mutane da yawa za su iya shiga cikin asusunka ba tare da sanin ka ba.

## Labari na 3

Ka samu saƙon imel ɗin da aka turo daga makarantarku, ana sanar da kai cewa an yi ma asusun ɗalibai da yawa kutse. Da'awar ita ce, "Kwanan nan mun gano cewa an shiga cikin asusun ɗalibai da yawa. Muna bayar da haƙuri kuma muna aiki damin mu gyara magance matsalar. Domin sake saita asusunka, ka ɗan bayar da amsa tare da sunan mai amfani da kalmar sirri ga wannan imel ɗin."

Abu ne da aka saba da shi kar a tambayi masu yin amfani irin wannan bayanin. Ko da kuwa mai aiko da saƙon ya yi kama da halartacce, ya kamata ka ɗauka cewa duk wani imel ɗin da kake neman kalmar sirrinka spam ne.

## Labari na 4

Ka sami wani saƙon imel daga bankin da kake da halartaccen asusu. Imel ɗin na cewa an yi masu kutse sannan kuma ka shiga ciki domin ka canza kalmar sirrin asusunka cikin gaggawa kuma ka canza kalmomin sirrin duk wani asusun da suke da kalmar sirri ɗaya.

Matakin da ya yi daidai shi ne a buɗe wani sabon window ɗin burauza sannan a shiga shafin yanar gizon kamar yanda ka saba shiga cikin sa. Irin wannan bayanin (cewa an yi ma asusu kutse) ana ambatonsa a kan shafin abokan hulɗar kamfani ko kuma bankin. Ya kamata a yi ƙokarin bin umarnin da ke kan shafin. Kamar yanda yake a cikin Labari na 3, babu wani halartaccen da zai nemi bayanin asusun daga gare ka a cikin imel.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.